Alƙiyama ba zata tashi ba har sai mutane sun dinga yin alfari da massalatai

Daga Anas - Allah Ya yarda da shi - cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: «Alƙiyama ba zata tashi ba har sai mutane sun dinga yin alfari da massalatai».

[Ingantacce ne] [Abu Dawud da Nasa'i da ibn Majah ne Suka Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana bada labarin cewa: Yana daga cikin alamomin kusancin ranar alƙiyama da kuma ƙarewar duniya mutane zasu dinga alfahari da ƙawata masallatansu, ko kuma alfaharinsu da duniyarsu a cikin masallatan da ba'a ginasu ba sai dan ambatan Allah.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/10897